# WIFI MOUSE DA YADDA AKE AMFANI DASHI

***Wallafar:*** Muhammad (CFRN) - 08096562396

*Website:* www.sharfadi.com

Email: info@sharfadi.com

*Facebook:* www.facebook.com/sharfaditeam

Twitter: www.twitter.com/bjournalist55

Instagram: www.instagram.com/basheer_sharfadi

Call & WhatsApp: +2349035830253




**#WifiMouse**

## Contents

**GABATARWA:** ....................................................................................................................1

**SHARADI:** ........................................................................................................................1

**MENENE WI-FI MOUSE?** ..................................................................................................1

**ABUBUWAN DA ZAKA IYA YI DA WI-FI MOUSE SUNE:** ...............................................1

**YADDA AKE SAITA WIFI MOUSE:** .....................................................................................2

**YADDA ZAKA SAUKE APPLICATION DIN WIFI MOUSE A WAYARKA**....................2

**YADDA ZAKA SAUKE WIFI MOUSE A COMPUTER DINKA:** ......................................3

**YADDA ZAKA HADA APPLICATION NA WIFI MOUSE DA KUMA COMPUTER DINKA**........................................................................................................................4

**YADDA ZAKA FARA AMFANI DA WIFI MOUSE:** ..........................................................6

**GABATARWA:**
Wannan littafi ne takaitacce da zai maida hankali wajen yin bayani akan Wi-fi Mouse da kuma abubuwan da ya kunsa, da yadda ake amfani dashi.

Cibiyar bincike da wayar da kan al'umma akan Internet ta ***Sharfadi.com*** ta shirya ta kuma tsara wannan littafi domin wayar da kan al'ummar mu kamar yadda ta sanya a gaba.

Cibiyar ta zabi harshen hausa domin gabatar da wannan littafi domin ganin ta bunkasa harshen Hausa a Internet.

**SHARADI:**
Ba'a yarda ayi amfani da wannan takarda ko wani bangare nata ba, ta kowacce hanya ba tare da izinin cibiyar ba.

**MENENE WI-FI MOUSE?**
Wi-Fi Mouse shine yadda zaka iya sarrafa computer dinka ta hanyar amfani da wayar ka ta hannu (Android ko Apple) a mazaunin mouse din computer, ko kuma keyboard, ko handle nayin game, ko kuma mayar da computer cikin wayarka.

**ABUBUWAN DA ZAKA IYA YI DA WI-FI MOUSE SUNE:**
1. Kunna audio dake kan computer tahanyar anfani da wayarka.
2. Canja audio,
3. Kashe sauti, kara sauti da sauransu.
4. Bude ko wacca irin folder, ko files a computer tahanyar anfani da wayarka.
5. Yin amfani da keyboard din waya wajen yin typing a computer.
6. Bude browser computer, batare da kayi amfani da mouse din computer ba.
7. Yin anfani da wayarka a ma zaunin handle din game a computer.

8. Anfani da wayarka wajan yin screenshot a computer.

9. Kashe computer (shutdown) ta hanyar anfani da wayarka

10. Duk wani abu da mouse da keyboard sukeyi itama wayarka zatayi.

11. Zaka iya fita waje da wayarka, kuma kayi operating computer dake cikin daki.

**YADDA AKE SAITA WIFI MOUSE:**

Wifi mouse zai baka damar sarrafa na'ura mal kwakwalwa ***(computer)*** ta hanyar anfani da wayar hannu ta android ko Apple.

Zamu raba wannan darasi gida uku kamar haka:

a. Yadda zaka sauke application din wifi mouse a wayarka

b. Yadda za kayi installing wifi mouse a computer dinka

c. Yaddda zaka hada wifi mouse din wayarka da kuma computer dinka domin fara aiki.

**YADDA ZAKA SAUKE APPLICATION DIN WIFI MOUSE A WAYARKA**

- Shiga manhajar playstore (google play)
- Kayi searching "Wifi Mouse"
- Kana kadanna install domin saukeshi zuwa wayarka.

**{Kamar Yadda Kuke Gani A Hoton Dake Kasa)**




## YADDA ZAKA SAUKE WIFI MOUSE A COMPUTER DINKA:

- Ka ziyarci adreshin wifi mouse kamar haka http://wifimouse.necta.us/
- Bayan ka ziyarci wannan adreshi, sai kayo kasa har sai kaga inda aka saka ***"Mouse Server"***
- Sai ka danna ***"Download"*** for windows.

**{Kamar Yadda Kuke Gani a Hoton Dake Kasa}**



Daga nan sai kayi ***Installing*** dinsa, zaka iya amfani da waya wajen daukowa sai ka mayar dashi kan computer dinka sannan kayi installing.

**YADDA ZAKA HADA APPLICATION NA WIFI MOUSE DA KUMA COMPUTER DINKA**

- Ana iya saita wifi mouse ta hanyoyi daban-daban, amma zamu tsagaita tahanyar ***hotspot*** da kuma ***wifi***.
- Ka kunna ***hotspot*** din wayarka, kana kayi hada (***connecting***) da wifin computer dinka.
- A kula sosai cewa ba sai ka kunna data ba, saboda wifi mouse baya anfani da data.
- Sai ka bude application din ***wifi mouse*** dake kan wayarka, zaka ga hoton computer tare da wani akwati mai numbobi masu dishi-dishi.

**(Kamar Yadda Kuke Gani A Hoton Dake Kasa)**




- Sai kadanna server dake kan computer, nanma zaka ga akwati mai numbobi ajiki anrubta i.p address (jerin numbobi)

**(Kamar Yadda Kuke Gani A Hoton Dake Kasa)**




- Sai ka shigar da wannan lambobin ***i.p address*** dake kan server computer zuwa wifi mouse dake kan wayarka.
- Sannan kadanna wani dan qarfe dake gefe.



## YADDA ZAKA FARA AMFANI DA WIFI MOUSE:

- Nan take zakaga abun mamaki kala-kala.

**(Kamar Yadda Kake Gani A Hotunan Dake Kasa)**

**WIFI MOUSE HOME PAGE**




**WIFI MOUSE APPS PAGE**





***Game Handle Controller***

Bamuyi bayani akan daukar computer chancakas zuwa cikin waya ba. Saboda wannan feature din sai mutum ya biya kudi.

***Muna maraba da tambayotinku!***

**Muhammad CFRN**

**Basheer Sharfadi**

**26/11/18**

**Research and awareness forum on Internet Sharfadi.com**